Imanin ɗayanku ba zai cika ba har sai son zuciyarsa ya kasance mai bi ga abin da na zo da shi

Daga Abdullahi ibnu Amr ibnul Aas - Allah Ya yarda da su - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: «Imanin ɗayanku ba zai cika ba har sai son zuciyarsa ya kasance mai bi ga abin da na zo da shi».

[Nawawi ya ce: Hadisi ne Ingantacce] [Mun rawaito shi a cikin littafin Al-Hujjah da isnadi ingantacce]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bayyana cewa mutum ba ya zama mumini mai cikakken imani na wajibi har sai soyayyarsa ta zama mai bi ga abin da Manzo - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya zo da shi na umarni da hani da wasunsu, sai ya so abin da ya yi umarni da shi, ya kuma ƙi abin da ya yi hani daga gare shi .

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/66535